*BINTA YAR JAGALIYA*

_story and writing_

_By_
Oum yasmeen

*🎃 wannan labarin ƙagaggene duk wanda yaga yayi dede da rayuwar sa to ya ɗauko a rashine sannan paid book 🎃*

Marubuciyar

*AFIF*

*YA ƊIN MAGE*

*RASHIN SANI*
MUZU BA MU GANI

Ƙarfe 4:50 pm

_____________Ƙasar limon garin kura tun daga baƙin lungun su yake ganin gungun yan siyasa da yake yanzu lokacin siyasa ne an kusa zaɓe

gyara babbar rigar sa yayi wacce duk ta koɗe jar shadda ce amma ta zama milk saboda zama a rana bawe sana'a yake ba aa yawon bara yake ƙafar sa na duba

Yawa wanda aka tono shi daga rami takalmin ƙafarsa ya ɗaure da leda

zuciyar sa ce ta ƙara tun zura ganin gungun yan siyasan nan sun fara ta fiya da alama sun gama taron da suke yi

takalmin ƙafar shi ya cire dan a cewarsa shi yake hana shi sauri har ya ƙasa ƙarasawa gun yan siyasar nan a hammata ya saka shi ya zura a guje yace

"Gwara inyi gudu domin Wallahi ba zan yi rashi biyu ba ga na wannan dan iskan yaron we shi

na matasa mai idanuwa yawa an soya gyaɗa shi yasa nake yin siyasar Alhaji datti mai tasa ,

Kash kafin ya ƙarasa har sun shiga mota sai sauran yan daba su ma kowannan su yana kama han yar inda zashi

gumi ya share ya nufi kangon gidan sa domin ko katanga babu sai langa langa a kasa tun daga ƙofar gidansa yake gano layin yan siyan a'wara koda ya ƙara miƙa huyan sa sai yaga ashe awarar ta ƙare mutanan da ya gani yan zaman hira ne annurin fusƙarshi ne ya ɗauke yace

"Wayyo Ni labahani tunda shegiyar yarinyar nan ta ajiye min shegiya a gidana na dena ganin samu sai de inga rashi to Wallahi da sake a gaskiya gimbiya ta cuce ni ta haifa min jaraba

ta mutu ta barni da ciwon ido dana zuciya yo ganin Binta yar jagaliya ai ciwon idone ka taɓa ya zame maka ƙamaya maya ka barshi ya hanaka bacci wasuma ce mata suke Binta yar daba ga shegen ƙarfi yarinya kamar ba mace ba tsiyar shege kenan ,

Ji yayi an roƙo rigar sa a fusa ce ya jiyo yawar ce kayar sa yace

"Malam lawandi kuturu na ce maka ka de na taɓa ni na lura nima so kake in kamu da cutar nan ,,

hannu sa ya kai kusa da hancin labahani yace

"Wallahi yazu na fara taɓa ka tun da na lura gudo na kake,,

Ganin lawandi da gaske yake yasa ya shiga gida a guje duk kayan da yaci karo sai yayi bal da shi uwani ce ta fito tayi ɗaurin ƙirji ta karka ta ɗauri gaba ta ce

"We Kai me isa malam baka tafiya a hankali ne duba fa kaga yar da kayi min jifa da kaya jifa jikin ka yawa wanda katafila ta baje ka ?"

I donsa ya kai kan kayan tuni yayi farin gani combos ɗin binta yar jagali ya gani a ramin gidan su wanda gun yazama kamar ƙwata tuni gumi ya tsastsafo masa a ransa yace

"Lalle yau na taɓo tsuliyar dodo ,,

Cikin kawar da maganar yace

"Uwani zan sami dan wani abu da zan sa a bakin salati ne ?"

hmmmm ina zaka sami wani abu tun da baka bayar ba ita yau me bayar War ta ce ta gaji

Uhmm kawe ya ce ya sami kujera yar tsuguno ya zauna ya zuba ta gumi domin abin duniya ya

fara isar sa tun safe yake baki titi daya ga yamma tayi suka haɗa kai shida abokin bararsa suka tafi gidan mai soyayyun idanuwa yawa an soya gyaɗa malam Shehu yace yana raba kuɗi kullum ga talakawa tun da uban sa ya tara mai shi kaɗe ya haifa gashi ya mutu shi ma yaron Allah yayi mai ƙashin arziki a she baya bawa mabarata sai wanda basu da shi dole ce ta sasu yin Bara koro su yasa akai a she da safe da ya fito ya gane su ya basu sadaka bazzawarar shi iyatu ta cinye tace sai min wannan tun da taga kuɗin ya ƙare tace mai rana tayi zata zagaya ko Allah zai sa wani ya bata sadaka

duba gabas tayi ta duba yamma tace

Tun safe tana ƙwace ko fitowa ba tayi ba sai dare yayi ta wanke ƙafa ta fita yawan siyasa kasan fa yanzu ya rinyar mai tasa ce dan majalisar tarayya jiya fa lado cemin yayi baƙar mota ce ta kawo ta we daga ƙasar limon take kasan fa na matasa ya zo garin nan campaign saboda shi yake son yaci zaɓen ƙasar nan ina zamu zabi gauro kofa auran fari beba ance we aljana ce ta aure shi mutum ya girma ga kuɗi ba aure

Jin karar buɗe ɗaki nayi da sauri na kalli ɗakin domin tun shugowa ta gidan ɗakin ya tsone min ido jine ance

"Kanbura uban can lalle yau akwai bidiri a gidan nan wanne shegenne yayi min hulli da takalmi na "

Kallon kallo aka shiga tsakanin uwani da labahani........✍🏼

BINTA JA GALIYA

Oum yasmeen

Chapter 11-16

_________Ganin sun yi shiru a lamar marasa gaskiya tace

"Magana nake kunyi shiru yau Wallahi sai na hana kowa zaman lafiya a gidan so nake ya bushe nan da ƙarfe tara in fita club shi ne a kai min tamola da shi ƙwafa tayi ,

Labahani hulal sa ya gyara yawa an kefa lutsassiyar tasa duk ta jeme koɗaddiyar rigar sa yasa ya share gumin fusƙar sa Wallahi yasan binta sarai wannan ƙaramin aikin ta ne ni labahani na shiga ya duk gimbiya ta jajamin ta haifamin jaraba gashi kaf mazan garin nan tsoranta suke ji balle ince  in zan Mata aure in huta duk magananar a zuciya yake yinta da bara ce ta faɗo mai da sauri ya tashi ya ɗauko ta ƙalmin ta ya ajjiye su da sauri ya ɗago jin wani uban kiɗa akan sa

Ayayye rass a nayi muna jin dadi sosai matashin yake rawa yana juya ɗuwawu kai ka ce mace ce ya ci irin kayan nan na wezaye

Cikin fusata labahani ya ɗauki ta ɓarya ya bishi a guje tuni matashin ya fara gundun cetar rai a bakin ƙofar gida yaji kamar ansa mai ƙarfe a huya zare ido yayi zai jiyo yaji ance

"Muje ciki oga ce ta bani umarni ka koma cikin gida in kuwa kaƙi Yanzu in maka billan barebari

Cikin rawar murya yace

"a'a ba batunƙi ai ni me biyayya ne a gare ku

muje ina ni ina billan barebari kaf dangina fulani ne muje nasan ni me laifi ne duk abin da yake ƙarfin haline domin shi baƙin sa baya mutuwa shiga yayi ya zauna a inda ya tashi

"Kahu labahani wa ya yimin cille da takalmi na har ya shiga cikin ƙwata sannan yanzu takalmin da nasiya sati ɗaya daya huce shi kai wa haka we yau she zaka de na shiga harkar kayana ji bi fa har leda ka saka mai duk ya fita daga kaman nin sa ?"

Wani irin gumine ya yan kowa labahani ai take ya tuna karon su da Binta cikin hikima yace

"Yar gidan gimbiya Wallahi bani da takalmin da zan sa shine na ɗauki naki amma ki haƙuri zan wanke in gyara miki shi ,

"Wanne ƙwallon shegenne ya yi min jifa da ta ƙalmin na kahu labahani?,

me ya faru kike zun duma wannan ashar ɗin ni kin ga yanzu na dawo daga nema ba abin da na samo ga uwar yunwa ina ji ?"

Juyowa ta yi nan na sami damar ƙare mata kallo baƙa ce amma ba can ba dan za'a iya kiranta da Black America bata da tsayi sosai dai tsayin ta dai dai misali ne bata da jiki sai de diri da Allah yayi mata domin ƙirjin ta cike yake dam ga hibs cikin ta a shafe yake yawa bata cin abinci

ko babu hanji a cikin ta ga dara daran idanuwa farare tas ga suma me kyau yawa komai ita tayiwa kan ta lips ɗinta pink colour baƙinta dan ƙarami saboda tsabar cikar girar ta har haɗewa take sexy eyes ɗinta ta ɗago ta dubi uwani

"Ni yanzu binta in tafi nemo abin da zan ci tun da kin gane bani da laifi sai ki tambayi uwani ko ita ta sani kai kuma matsamin da ga kai da fusƙar ka yawa anyi ɗaurayar zunubi.... ,

cikin jin zafin maganar sa yasa dan daban nan ya zaro huƙa yace

"Yasin in daba dan darajar ki ba da tuni da daɗe da sumar da tsohon nan ,

Wani kallo Binta yar jagaliya ta watsa mai domin duk yar tsamar dake tsakanin ta da kahun ta bata bawa wani ƙofar cin zarafin sa ba

Cije baki yayi yace

"Yi hakuri oga dawa dai dawa an buga dake anbar ki maƙiyan ki fadawan ki kinci dubu sai ce to ke murucin kan dutsai ce baki fito ba sai da kika shirya,

Gyara rigar sa yayi yace

"In tafi Binta dan girman Allah ƙarki saƙar mana muciji a gida Wallahi shegaran jiya da ya naɗemin huya ko bara ban fita ba har gudawa nayi a zaune kai kuma a haka zaka ƙare kana cije baki yawa wani maye ,

banza tayi mai domin ta tsani barar da yake zuwa tace

"Wa ya yimin wulli da combos ɗina ?"

Ɗaurin ƙirjin ta ta gyara tace

"Yo ina zan sani kina ga fa tun da na gama aikin tatar koko na koma ɗaki na kwanta kuma kin ga meragaje bata dawo ba tana faɗar haka ta shige ɗaki ,

Hmmmm kawe binta tace

Hamdallah labahani yayi ransa Allah ya temake shi bashi da rabon huya domin yana tuna karon su na bara be jindadi ba kare tasa yayi masa kaca kaca da katifa kai kace markaɗata a kai a inji

shi a haka dadi yaji da bashi suka yagal gala ba tashi yayi domin tun da ansa mu tayi shiru da zancan gwara ya fita waje ya nemo abinci da ya tambaye ta lamarin ya ƙara caɓewa

Kujerar da ya tashi ta zauna tana kar kaɗa kafa yawa wata sarauniya yana nufar soro a guje ya

dawo a she binta kwantan ɓouna ta yi mai ɗane kan bishiya yayi tuni karun nuka suka za gaye bishiyar suna

haushe gashi ko za'a kwana a yini inba tayi musu magana ba baza su bar shi ba

Ƙibƙibta ido ya fara domin yau yasan me raba shi da Binta yar jagaliya sai Allah ba bakin sa ya buɗe a walale yace

"Binta kiwa Allah da Manzonsa ki barni haka ,

Jikin ta ne yayi sanyi yasa tace

Cleaner,reza ku zo tuni suka tawo gunta a jiyar zuciya yayi ya sauko

*KURA GOVERNMENT HOUSE*

Yanzu yaya kuke ganin za muyi da yaron nan ya taso da masoya ya za muyi mu batar da siyasar sa ni Wallahi har far gaba nake gani nake Kamar ba zan koma kujerar mulki na ba

Honourable Nasir yace

"Haba excellency me akai kayi shi duk da ya sami ɗaurin gindi a gun kakan sa amma Wallahi ba zai kai ga ci ba kana ganin al'ummar limon za su zaɓi gauro ne ba shi da aure fa,

Alhaji datti mai tasa ya ce

"Ku barmin ku mai a hannu na zan sa sojojin baka su ɓata shi a gidan Radio da social media ni Wallahi ko yanzu na sami dama sai na kashe kura domin tsohon nan ya tsaya min a rai ,

Excellency yace

"Ko ni dama nake nema in ban zama shugaban ƙasa ba to Wallahi sharrin kura ne ,

Ƙar ku damu ina da Binta yar jagaliya ku ɗauka yawa anyi an gama

dukan su dariya suka sa domin sun san binta yar jagali ba ƙanwar sala bace

Wannan kenan

Kallo ɗaya za kai wa tsohon kasan hutu da jin dadi sun zauna kuma za kasan tsohon dan siyasa farine tas shi yasa a lokacin siyasar sa ake cewa sukari bakai farin banza ba kai bangon sukari ne kowa ya jin gina da kai sai ya sami arziki yana yi dim tawa al'umma shi yasa yanzu yake so jikan sa ya gaje shi badan komai ba sai dan cin hanci da rashawa sun addabi al'umma

musamman wannan gwamnatin me ci a yanzu

ya ruƙe muƙamai da dama har yakai matsayin shugaban ƙasa yanzu da ba mulki sai ya dawo gidan sa dake garin taura yana zaune cikin yan uwa da abokan arziki ba kowa ne sai

*Alhaji Ibrahim Bashir kura* duban jikan sa yayi yace

"Azzaman naji yan jarida suna so suyi hira da kai ?"

a hankali ya ɗago kan sa da sauri nayi ƙasa da nawa idon saboda kwarjininsa da ciƙar kamalal sa

farine tas yawa Balarabe babbane amma ba can a ƙalla zai kai shekara talatin da tara yana sanye cikin manyan kaya yadin kubta ne a jikin sa brown colour anmai aiki da milk colour irin na sarakan nan fusƙarsa cike da ƙasumba kwance lub hulal sa ya cire yayi aski sama sama cikin husky voice ɗin sa yace

"Eh baffa amma har yau banyi approval ɗin ta ƙar dar ba ,

Lumshe idon sa yayi yace

"Kai abu me kyau sosai sai na gab da primary election sannan sai ka fara baza manufu fin mu ɗazu a bu gomin yawa su mai tasa sunyi taro a kan rusa ka kabi a hankali sannan ka iya ta ƙunka sannan dole ka bar gidan ka na j.r.a kadawo kura estate ɗin nan mu zauna tare ,

Cire farin glass ɗin sa me kama da medical yace

"insha'Allah Zan kiyaye sannan zan dawo,

Cikin ƙausar murya ya ce

"Mu'azzam mu'azzam mu'azzam dole ka fito da matar aure kar ka ɓarar min da abubuwan da na shirya wa ƙasar nan nasan wannan dalilin ne zai sa a ƙi baka takarar ka kasan ko su yanzu da wannan suke ganin za su rusaka sannan wannan yarinyar yar social media nasan zaka iya ganin ta musamman wannan ƙafar ta Tiktok nasan zaka iya gani tallata dan takarar shugaban kasa wato sunusi dalhatu mai rawani gwamnan garin nan tana da mabiya da yawa amma tambas ta taɓo mu wallahi Wallahi Wallahi sai na shafe ba bin ta dole ta zamu ƙar ƙashin ikona ko naka ? ,

Da sauri ya ɗago manyan idanuwan sa domin ya girgiza da zan can baffan sa

Gyara zaman sa yayi ya ɗora ƙafa daya kan ɗaya yace

"Eh kai a kwai wani shiri da nake yi in har ta kus kura ta taɓo mu ta ƙarɓi kwangilar rusa mu,

Hmmmm kawe yace domin yasan sarai kakan sa baya maganar banza

Sannan ina so kayi fallowing ɗinta zaka ga user name ɗin ta princess Fatima zarah

"Baffa ni kuma inyi fallowing ɗinta ?"

Eh kayi zaka ga irin abin da take yi duk da bata shigar ban za sai dai rashin kunya sannan zan sa aimin bincike a kanta

Hanky ya ɗauko ya goge fusƙar sa yace

"Zan buɗe wani account ɗin amma ba zan yi da nawa ba zata ɗauka ita wani abun ce ,

Sosai tsohon shugaban kasar yayi wata dari yace

"Good idea tambas Bilal ya haifamin copy na me kama dani me suna na Allah ya jikan sa da rahama,

Ameen baffa tashi yayi ya mai da hulal sa ashe dogone ga kiba ya zura wayar sa a aljihu yace

"Zan tafi limon yau saboda jikin Hajiya ta ciwon ta ya ta shi ,

Allah ya bata lafiya ka ce ina mata sannu sannan kace................✍🏼

*BINTA YAR JA GALIYA*

*

Bourn page

"Ta fito da kuɗi ki manin biliyan hudu za muyi campaign da su nan da wata me kamawa,

Kallon kakan nasa yake cikin rashin fahimta yace

"Baffa biliyan hudu fa bata yi yawa kasan fa ita siyasa mace ce me ciki ba a san me zata haifa ba ?,

Azurfar hannu sa ya murza ya ɗauki limon tatatcan inibi ya sha ya ajjiye akan Centre table yace

"A dukiyar mu in mun ɗauki biliyan hudu kamar mun ɗauki naira biyar ce hidimtwa talakawa mukai ko mun rasa ba baƙin ciki,

Azzam yace

"Hakane baffa Allah ya sa mu dace sannan dan Allah baffa ƙar Musa yan daba a siyasar mu sai ma mu jawo su a jiki muga sun shiryu sannan in na hau mulkin kasar nan zan kama duk wani wanda ya ke siyar da kayan shaye shaye da dilolin sai na kama su,

Yayi kyau Allah ya temaka

yace

"Ameen"

ya fita gida ne babba ya tsaru ga jami'an tsaro sai zagaye su ke inda yayi parking motar sa ya nufa cikin sauri driver sa ya jiran sa ya buɗe mai gidan me zaman banza ya shi ga

"Oga ina zamu?,

Shiru yayi na wasu sa ƙanin san nan yace

"Kura international airport ,

Musa driver yace

"To,

driver yace domin in da sabo ya sama da halin sa tun mahaifin sa na da rai shi yake kai shi ko ina yanzu shekara goma sha bakwai yana tare da shi yana jin dadi aiki da shi yana girmama tsofan sa hawa kan lafiyayyan titin da zai sada shi da airport da yake yanzu gari yayi duhu an

kusan magarib sosai ya buɗe ido yake ganin komai na garin kura sun zo kusa da government house  gani yayi an tare hanyar ana taron siyasa ga yan shaye shaye da yan daba sun tare hanyar suna ta busa hayaƙi

Kau da kai yayi yace

"We yau she za a de na wannan siyasar ne ?"

Aikuwa wannan siyasar gari nan sai addu'a

Allah yasa mu dace

"Amin ya Allah ,

Ammasu mai tasa sun lalata ƙasar nan

Shiru yayi yana ɗan ne a wayar shi shaf ya manta da zan can yayi fallowing ɗinta harka business ɗin sa yake isa airport sukai nan da nan aka yi mai tarba me kyau sai nan nan ake da shi prevent set aka kai shi nan jirgi ya tashi sai ƙasar limon driver sa ya yo  gida da motar da yake shi kaɗe zai je ban da shi headphone 🎧 yasa a ƙunnan sa bawe waƙa zai jiba a'a karatun Alkur'ani mai girma yake ji lumshe idanuwa yayi yana sauraran a hankali  yake motsa labɓansa yana bi a hankali har suka iso ƙasar limon a hankali yake tattaka stairs case ɗin jirgin yayin da brief case ɗin na hannu zan wata kyakkyawar motar baƙa har ta glass ɗin baƙi ne yar gidan Benz ta tsaya a gaban sa

 security ɗin sa  suka tare shi saboda irin ciƙar da akai a waje tarbar sa sosai ya shiga mamaki saboda shi be sanar wa kowa zai zo garin ba tuni security suka shiga tare hanyar shiga cikin sauri ya shiga mota driver da Hajiya ta turomai ya ja shi yana fita sosai mutane suka rufe shi hannu ya ɗin ga ɗaga musu ganin irin soyayyar da suka nuna mai

 ya ciro kudi wanda shima besan a dadin su ba ya ɗin ga watsa musu har ya samu hanya jilibal j.r.a ya nufa da shi unguwar wance da wane duk wanda kagan shi a unguwar to yaci ya tada kai anan zone 1 nan faɗar shugaban ƙasa take shi kuma yana zone 2 a gaskiya iya tsaruwa limon ta tsaru yawa a ƙasar waje kake jami'an tsaron sai yawo suke da bindigu tsayar da su Ku kai katin shi ya ɗauko na shedar shi ɗan cikin gun ne yasa suka barshi ya shiga amma ko tsutsune ba su yarda da motsin shi ba sai sun harbe shi da yake ba sabo kullum da irin wa'yanda za'a kawo

gaban wani tamƙameman gida suka tsaya sojojin dake tsaron gidan suka buɗe mai suna sara mai da yake mahaifin shi babban soja ne lokacin mulkin soja ya ruƙe kasar na shekara bakwai bayan ya sauka farar hula ta ƙarɓi mulki tun da lokacin soja be ƙara ƙar ɓa ba har kawo i yau gidan girma gare shi ga an ƙawata shi

Kai kace wata ɗaulal ƙasar larabawa kake parking space suka nufa yana dai dai ta tsayuwar motar sa ya fito a cikin nutsuwa yake tafiya har ya isa ɓangaran hajiya Turai tsayawa a kwatanta ƙyan gun ɓata baki ne sallama yayi

cikin fari'a yar shekara sittin taci doguwar riga ta tsadar diyyar atamfa tayi dauri irin maryam a bacha

hannayan ta tayi jan kunshi wata budurwa ce a kusa da ita ƴar kimanin shekaru goma sha tara taci fitted gown ta wani material baƙi an mai adon flower golding colour hannun ta ruƙe da tamfatsi tsiyar waya tana video a tiktok ganin sa yasa ta ƙasai cikin ƙissa tace

"Your welcome back my big brother,

ɗur ƙusawa yayi ya zauna a lallausan carpet cikin girmamawa da ƙaunar mahaifiyar sa yace

"Barka da dare hajiya da fatan na same ki lafiya ,

Tace

"Lafiya qalau alhmdllh da baka dawo ba na sami sauki kwana biyu na ci gishiri ne shi yasa hawan jina ya tashi ,

Allah ya ƙara sauki

"Ameen azzam baka ga yusrah ba ?"

Cikin nuna tsananin biyayya ga mahaifiyar sa yace

"daman bata koma ba?,

Eh ta dawo nan saboda zama ni kaɗe ba dadi ga kai kaƙi aure balle in Sami jikokin da zan ɗin ga gani suna ɗebe min kewa su ramlat suna nan zuwa suma

Shiru yayi domin beji dadi ganin Hajiya Turai tayi zance auran sa a gaban yusrah

Ga abincin ka a dining room ko sai kayi wanka ne

"eh ga magarib an kusan kirawo wa ,

Okay a fito lafiya

Ameen ya ce ya tashi ya nufi wata ƙofa inda ta nan ne zai isa shashin sa yana shiga bedroom ya nufa ya cire kayan sa ya shiga toilet wanka yayi ya fito ya shirya cikin jallabiya brown colour ya feshe jikin sa da tsadaddun turarurruka masu kyau da tsada tuni yake fidda ƙamshi me dadi counter din sa ya ɗauka ya fito a hankali yake motsa baƙin sa yana tasbiyi sai ka kula sosai sannan zaka gane baƙin sa na motsi central mosque ya nufa

masallacin fadar shugaban ƙasa da yake an kusa kiran sallah da yake ba jami'yar su bace ke mulki sun gaisa da abokan hamayya sun gaisa cikin mutunta juna

(Wani abun sai mu talakawa in mutum baya jam'iyyar da kake ka dau gaba da shi kenan har abada wani har jafa'i kake jamai mu dena yarda masu mulki suna gwara kanmu alhalin su nasu a haɗe yake siyasa daman ita mugun wasa ne)

Sai bayan sallar Isha'i ya dawo gida kai tsaye dining room ya nufa abinci ne sunfi kala goma ajere da sauri yusrah ta taso ta cire rigar dake jikin ta yan zu doguwar riga ce me roba duk ta bi jikin ta ga uban farce da tasa yawa me shirin shan jini tace

"Bara inyi zuba maka ,

Da sauri ya ɗaga mata hannu ya nuna mata hanya

Wasu kwallace ne suka toro a idon ta ga yahun bakin ta da ya ƙafe jiki a sanyaye ta juya tana juya ɗuwawu

taɓe baki yayi domin ko a jikin sa  shi yana mamakin yan matan yaxu su dinga yiwa maza tallan kan su lemon kwakwa ya zuba ƙadan sai farfesun hanta wanda yaji albasa da kayan ƙamshi ya zuba kanda ya fara ci

bayan ya gama ya ɗauki tissue ya goge bakin sa ya nufi bedroom ɗin Hajiya Turai domin yi mata sallama akan daduma ya yatarar da ita tana addu'a zama yayi a ƙasa suka shafa tare yace

"Hajiya sai dai safe,

Cire hijab ɗin ta tayi tace

"Har ka gama ?"

Eh zan je in ƙwanta gobe zan je store ne saboda a ƙwai sababbin kayan da nayi order to sun zo tun waccan satin ina so in rabawa yan kasuwa ne be dace in roƙe Kaya ba bacin ana nema

Hakane Allah yayi albarka ka

Ameen baffa yace ki fito da kuɗi kimanin biliyan hudu

"To, kawe tace mai

Tashi yayi ya nufi shashin sa shirin kwanciya yayi kasan bacci yasan ya kashe lamp ya mai da dum light yayi addu'a ya kwanta ya ja blanket ɗin sa ɗaya wayar shi ya ɗauko ya buɗe tiktok ya nemo sunan ta duk wani video nata iya fusƙarta kawe take nunawa tsaki yayi yace

Allah ka rabamu da fitinar zamani ka mar a mafarki yaga yusrah ita da wani namiji suna kiss ɗin juna sosai hankalin sa ya tashi

Wannan kenan. 10:30 pm

Zabga ƙamahi take kai kace ɓarin turare tayi a kayanta abaya ce baƙa yar Turkiyya sai taunar chengum ta ke ba kwalliya a fuskar ta amma tayi kyau mayafin a bayar ta sashi a kanta kashin kanta ya sha gyara kowa sabgar gaban sa yake a gun masu shaye shaye nayi masu soyayyar shan minti nayi masu rawa nayi masu shan shisha hayaƙi ta ja ta fisar tace

"Wallahi Binta kina ban mamaki ya kamata ki amince da muƙatar Alhaji kin san kuɗi ba matsalal shi bace ,

Dena danna wayar ta tayi tayiwa ƙawarta ta banzan kallo tace

"Rufy bani da wata daraja da ƙima sai wannan mutuncin nawa ba zan rabawa kadangarun bariki ba insha'Allahu sai na kai shi gidan mijina yar da zai kalleni da mutunci sannin kanki ne kinsan mumsa kanmu a wahala duk wani mutumin arziki baya kallon yar tiktok a matsayin me mutunci wasu ma kallon mushurukai suke mana dan haka

Wallahi ƙar ki ƙara yimin wannan zanca balle ni da duniya ke kallo na karuwa ga shi wannan najadun tsohon ya ƙara zubar min da mutunci yau Wallahi su nusi sun shiga ukku we harni zasu yiwa kahu video yana Bara sun sa yace ni yar sa ce bana bashi komai shi yasa yake bara shi yasa yau ko Kabo na ban bayar ba sun bashi kuɗi dan su cimin mutunci,

Gaskiya basu kyauta ba

Hango su tayi da sauri ta tashi ta nufi tabirin giya ta fasa ɗaya ta nufi kansu tuni komai ya tsaya aka kashe kiɗan saboda ƙar fasa ƙwalba da a kaji wayan da suka dade basu zo club ɗin ba yau

sun zo domin sun san a kwai drama tun har neman magana yasa su nusi suka taɓo yar gaban goshin gwamna.........

*

Bourn page

Cikin sauri rufy ta kamo ta cikin Muryar wanda ta sha tayi manƙas tace

"Haba sister wannan ba girman ki bane kina da yara kisa suci uban su me akai akayi su nusi ko followers 1k basu da shi sun taɓo kine dan ki kula su suyi suna ,

A jiyar zuciya ta sauke ta yar da ƙwalbar a ƙasa ta ɗauki jaƙar ta rataya ta dubi nusi tace

"Za mu haɗu ko ba a nan ba kin san bana barin bashi ƙaramar arniya ki bari sai kin kai sannan sai ki taɓo ni ƙanne mata ido ɗaya tayi ƙas da hannu,

Wani irin ihu gun ya ɗauka suka ci gaba da rawar su

Ita kuwa fita tayi ranta a ɓaci jin horn tayi da sauri ta juyo

Wani matashi ne ya ci asƙin nan na yan isa ya leƙo da kansa yace

"Hey Beb how you doing ?,

Cikin ɓacin rai ta buɗe gidan gaba ta shi ga ta saki a jiyar zuciya ta biyu tace

Jazzz kai ni gida raina a ɓace yake

Wata ƙwalba ya ɗauko yace

Kullum ina faɗa miki in kina shan wannan ba ke ba ɓacin rai

Cikin I don't care manner tace

"Jazzzzzzz Please ai sai ɗauƙar hakki yayi yawa ƙarshe in shaye shaye yayi min yawa in hauka ce ko ? to ba haka nake ba nasan mutuncin kai na ,

Murmushi yayi yasa

waƙar simi me taken love don't care ya saki ya fara tafiya a hankali yana bin waƙar juyowa yayi yace

Okay Alhaji datti yace min
yau 12:00 ki same shi a government house

Ɗa gowa tayi tace

"I don't have any time,

Da katawa yayi da bin waƙar yace

"Why not?,

Banyi niya ba kasan we yana so in ƙarɓi ƙwangilal ɓata wannan pro 'azzam Bilal mu'azzam kura

Kina tsoron sa ne

Dariya tayi tace

"Ko ɗaya sai de ina tsoron Allah kasan fa sharri zan mai ,

Dariya yayi har da ruƙe ciki sai da ya gama sannan yace

"Beb tsoron Allah fa kika ce ai Wallahi da gani har ke ba batun tsoron Allah a rayuwar mu kin san kafin izo nan daga ina nake hmm Allah ya kyauta na birni ya cuci na ƙauye ,

ai kasan duk iskancin mutum akwai wan da ya fi shi wata ƙila kai kafi ni

Hmmmm kee uhmm ai Wallahi ko bokan daji haka ya ganki ya ƙyale

Wani kallo ta yi mai tace

Uhmm haka kake gani ni Yanzu so nake in zub da makaman yaƙi na gaji Wallahi

"Ya kamata in karatu ne in roƙe kalaman ki sau nawa kike faɗar haka,

Rufe sexy eyes ɗinta tayi tace

"A kwana kin nan Wallahi ina yawan yan mafarkai ko da na tashi bana gane komai ina tsoron wani abu ya faru fa bana ganina a wannan duniya a wata daban nake gani na fa ga wani mutum bana iya ganin fusƙar sa sai de bayan sa ,

"Hhhhhhhhh ko suruki na ne?,

Hmmmm ka dena daukan magana ta wasa jazz

"To Allah ya kawo mafita,

"Ameen,

zo muyi video yau in rikita fans ɗina kin san wasu cewa suke we bakƴa video da namiji

Hmmmm kawe ta ce

Iphone 15 ya ɗauko ya shiga tiktok yace

Hey fans gani ga Princess bintu

Murmushi tayi tace

Hey fans yau gani ga jazzzzzzz nan yasa musu waƙar salim smart me taken labarina baya zama nawa inhar bake tariyi na sukai bi waƙar dai dai gidan su ya tsaya yace

''beb gobe in dawo ?'

Ba zan fita gobe ba

Okay bye

Bye fito wa tayi tsaki ta ja ganin yan zaman sha isaka da yake zafi ake suna zaune suna hira da munafurci canza taku tayi tafiyar ta tayi sai ƙas ƙas taƙalmin ta keyi

Wani daga ciki ne yace

Allah ka shirya mana zuri'a

Juyowa tayi ta ɗage glass ɗin ta sama tace

"Amin dan karuwa uban ka yasa kwabashu me huta ,

Tuni sauran sukai shiru domin sun san tsaf zata zage su

shiga soron gidan su ta shi ga ta ƙunna fitilar wayar ta da yake ba huta  da sauri ta tsaya ganin meragaje da saurayinta ɗantala suna manne da juna cikin ƙunar rai tace

Dan uwar ka a she baka da hankali tunda har ka iya zuwa gidan mu kana nema ka lallata meragaje rayuwa

Jikinsa rawa ya fara yace

Dan girman Allah ki haƙuri

Uhmmm ke kuma shiga gida ko inyi kasa kasa dake  kai kuma zamu haɗu a way zanyi maganin ka

Ki yi hakuri

Baza tayi mai

Meragaje ta shiga gida da gudo tana kuka

Cikin sauri uwani ta fito tace

Meragaje lafiya kike kuka

Koroni tayi muna tare da ɗantala we zai lallatani

Kan uban can ita daga ina take ke gwara kina gida ita fa

"Daga gidan uban ki ,

Hantar cikin uwani ce ta kaɗa batayi zatan zata jiba ta zata ta  tsaya suyi tujara da ta saba ashe ta shigo

cikin sauri ta kama hannun Meragaje suka shiga ɗaki

Kama ƙugu tayi jin alamar ringing a jaƙar ta da sauri ta ɗauka ganin sunan yasa ta ja ƙaramin

tsaki ta ɗaga tayi shiru

"Haba Binta kin sa fa dake muka do gara na tabbata in ki kayi wannan aikin Wallahi za mu sami kujera kin san fa ni zan fito ta karar gwamna nayi miki alkawarin biliyan shidda har da mota wacce ba kowa ke hawan ta ba,

Shiru tayi ta shiga tunani anya kuwa za ta bar kuɗin nan tana da buƙatar nemo mahaifin ta saboda rashin kuɗi

bata sami zuwa Saudiyya ba domin mamanta har address ɗin sa ta bata kawar da wannan tunanin tayi tace

Amma Alhaji datti baka ganin duniya zata zage ni sannan taya zan kulla mai sharri har a yarda

Wata irin shu'umar dariya yayi yace

Wannan ba matsala bane domin kinsan na iya kulla sharri da maƙirci zamu kulla mai gadar zare kuma keee zaki je zan baki karamar camera ki sa a jikin ki tunda Allah yayi miki halitta da zaki ɗauki hankalin duk wani ɗana miji in de me lafiya ne

Samin gu tayi ta zauna tace

"Alhaji tsiraici na zaku nuna wa duniya akan mulki tab Wallahi da na san Wannan banzar maganar zaku zomin da ita Wallahi da tuni na daɗe da dena harka da ku kai hmmmm,

Kin daka ta kiji mana ko fusƙarki ba wanda za a nuna sannan kuma za'a rufe jikin ki kawe hugging ɗin sa zaki yi kin fahimta sannan sai kinyi taka tsantsan muna sakin video nan zaki dawo gidan gwamnati da zama

Okay na yar da

Yauwa ko ke fa kashe wayar tayi ruwa ta ɗiba ta zuba a buta ta nufi bayi bayan ta fito ta tora ƙofar ɗakin ta da sauri ta kunna fitilar wayar ta wa zata gani cikin baƙin ciki tace

"Kut melesi jajar uban can Wallahi yau kowa ba zai bacci ba jajar uban can lalle ,

Iya da take sharar bacci bata san wacce wainar Binta ke toyawa ba

A fusace ta fito ta fara dukan ƙofar ɗakin kahu labahani

Cikin magagin bacci yace

Wane mara neman albarka ne yake tashi na tun asuba da na fita nema ban dawo ba sai hudu

Wata da bara ce ta haɗo mata ta maƙe murya tace

"Fatalwa ce ,

Cikin ɗaki kuwa tuni wani irin tashin hankali ya ruske shi Oni labahani a haka mutuwa ta zo ban cika burina ko  ɗaya ba a duniya ashe a fili yake

Gyara tsayuwa tayi tace

"Ai kuwa yau zaka baƙunci lahira domin mun gani ana ta'asa a gidan ,

Dan girman Allah fatalwa kiyi min rai Wallahi ban sani ba cikin yar da bara ya sa ƙafa ya doka a wa uwani domin Wallahi ba zai fuskanci tashin hankalil nan shi ka ɗe ba yace

"Uwani tashi  daman ance in da rai zaka sha kallo yau ga fatalwar gimbiya nan ta dawo kan mu,

Aikuwa cikin masifa ta ɗauko tasar da taci abinci ɗazu ta buga mai tace

"Zan fasa maka kai kafin ni ka fasamin fatsarmama in ban da ka mai dani mara hankali fatalwar gimbiya ce  za tazo gidan nan?"

*Ya ku yan adam har kuna da lokacin yin faɗa alhalin yau zaku mutu*

Innalilahi dan girman Allah ai bansan gaskiya yake faɗa ba kaimin rai Wallahi bacci nake ya ta sheni

Ai kuwa yau zaku yi kwanan barzahu

Tuni uwani ta saki gudawa a zaune yayin da numfashin labahani da ƙyar yake fita saboda ta shin hankalin da yake ciki ko mutsi ba yaso yayi ƙoƙari yake ya tuno addu'a amma ina ya kasa

sai mun jaye nu'ara kulya li'ilafi  yake mai mai tawa tun yanayi ahankali har ya dawo da ƙarfi...........✍🏼

*BINTA YAR JA GALIYA*

free page

Dariya ce ta kusan kuɓucce mata ta danne tace

"zan baku zaɓi ku zaɓa in kuna so in barku da ranku sai kun hana saurayin meragaje zuwa gidan nan in da gaske yake ya fito ya aure ta

ko in  hana ku ba haya na tsawan shekara ɗari ko in saƙar maka gudawa ta tsawan shekara tamanin ,

zaro ido yayi tuni wata gudawa ta kuɓucce mai ji kake tsuuuuuu yawa an saki fanfo   taɓa ƙasan shi yayi  ga wani irin wari da ya game ɗakin a zuciyar shi yace

"anxu gun har an fara saƙar min tawa yasan wataran ba gudawa zaiyi ba sai de ya kashayar da ƴa'yan hanjin sa  ,

duban uwani yake amma a baɗini wasu taurari yake gani sun za gaye shi yau yasan ƙar shan sa ya zo shekara ɗari ba kashi ko ƙwana ɗaya mutum beba yake ji  balle mutum yayi shekara ɗari

futsari ne ya biyo baya jin har da gudawa yo rana daya mutum yayi gudawa yake fita hayyacin sa balle shekara tamanin ai kawe mutuwar tsaye zaiyi da kyar ya iya buɗe baki yace

Innalillahi fatalwar gimbiya ku yimin  min rai dan allah wallahi ba laifina bane laifin uwani ne na matsani yaron nan ita ta dage sai ya zo gun mairo

Zuface ta ƙaryowa uwani tace

Wallahi sharri yake mun kullum sai ya bashi kuɗi ko mero

MERO da ta fita hayyacin ta tayi dana sanin shigowar ta ɗakin nan tace

"Eyyy eh wayyo allah,

banzan kallo labahani yayi mata yace

"tsakani na da gimbiya a ƙwai ƙauna ta gaskiya da amana kowa na garin nan ya sheda,

FATALWAR GIMBIYA ni na zaɓi na farko zan hana shi zuwa

a'a ke naki da banne waccan tsohowar da ta kwanta a ɗakin binta zaki taso ta sannan ƙarta ƙara ƙwana in ba haka ba mu shanye muku ƙafafuwa ke da ita

"To, zan taso ta insha allah haka baxata faruba ,

Duk da  halin da yake ciki be hanashi zabgawa uwani wata uwar harara yace

"hmmmm ai duk ke kika jamini saboda san ƙuɗin ki shegiya me subfar ƙaguwa ,

"kun ceci kan ku ni zan tafi chaina ,

Ɗif suka ji da sauri uwani ta tashi ta fito domin tada iya mahaifiyar ta da tazo daga ƙauye

da gudu binta ta waɗa ban ɗaki cikin ta har murɗewa yake saboda dariyar da ke cin ta in bahaka tayi ba iya ba zata fitar mata daga daki ba in tujara dake ji da ita to iya tafita

Jin alamar gudu yasa uwani ta dafe kanta domin a tunaninta fatalwar gimbiya ce ta tashi sama domin ƙarta warce mata kanta yasa ta dafe shi

"IYA IYA IYA ,

sosai tsohowar ke sharar munshari har da yahun bacci

Hannu uwani tasa ta buga matashin iya a fusace iya ta sa hannu ta buge hannun uwani tace

Dan allah ku barin na huta tun ɗazu kuke ta shina yawa wanda na ciwa wani bashi

"hmmmm iya yau fatalwar gimbiya ta zo gidan nan ɗazu ta tafi wallahi tace ƙar ki ƙara ƙwanciya a ɗaƙin ƴar ta in ba haka ba sai ta shanye mana kafafu,

cikin sauri IYA ta tashi ta zabgawa yar tata harara tace

Owani lami me yashin madina  ƴar da na haifa da cikina ita ke sharara min ƙarya uwani bura'uban ki uwani na yi miki kama da wacce fatalwa zata ambaci sunan ta to yasin har in bar gidan nan a ɗakin nan zan ƙwana

Wasu hawayene masu yaji suka zubu a idon uwani tace dan girman allah iya ki zo mu tafi ƙar suji ja'in jar da muke da ke

zani ta gyara ta fyace majina ta sai ta matashin ta ƙwanta  tace

Alƙur'an uwani ki fita adona in rufe wallahi uwani ina raga miki da iliyane da tuni na zubar mai da haƙura ai ɗazu itama shegiyar ina jinta nayi mata shiru domin ban zo gidan nan in ƙwanta a tabarma ba nazo inji laushin katifa ai gashi ta haƙura ta fuce tasan duk tujararta na fita hhhhhhh gaba da gaban ta aljani ya taka huta

majina uwani ta face ta haɗa hannuwanta biyu tace

"IYA dan girman Allah ki haƙuri ki taso mu tafi ,

wata uwar ɗirga sukaji a lamun abu buwa sun  sauka tuni hanjin cikin uwani ya cure gu ɗaya ta fara zare idanuwa domin ba baƙin magana IYA ta ja musu da ta taso da duk haka bata faru ba

"wani irin ƙugi su kaji guggugug wata ku bil adama kuna da taurin kai na baku dama ku fita ƙunƙi gashi ni har naje chaina na dawo kuna zaune ,

zaro ido IYA tayi ya dafe ƙirji daman tun zuwan uwani da ta bita Allah sarki ashe sona uwani ke yi oni lami na shiga ukku yau sai ta Allah tace

*"UWANI* in kin sami kuɓuta ina bin matar me gari naira hamsim kuɗin daddawa ki amso kiyi min sadaƙar ashirin da biyar sannan ki gina min masallaci da raguwar kuɗin tun huri na keso in

iya sa'alun amma sakalci na ya hanani

yanzu da tayi min rana ina zuwa ƙabari ana tambayata in amsa kuka tasa domin ba haka ta so ba taso abar mata jiran duniya ,

zuba mata ido uwani tayi da alama IYA  ta fita hayyacinta bata san me take faɗa ba yanzu har yaje chaina ya dawo ji tayi fa a radio ance ba ƙasar da takai chaina nisa

"ɗazu na ƙafa muku sharaɗi kun bujere min to zaku rufe idanuwan ku har sai wani daran yayi sannan ku buɗe in kuka ƙus kura kuka buɗe to fa rundunar aljani gushshu zatayi sama daku sannan ki faɗawa labahani ƙar ya sake ya ƙara fita waje da sunan bara sai de yaji anyi sama dashi bashi ba dawowa,

"To mun gode ,

tuni suka rufe idon su suka fara laluban ƙofa ruge ruge suka shi ga yi  ganin uwani ta bangaje IYA ba ta luraba yasa IYA ta fusgota ta dawo da ita baya tayi wuf ta futa gani take in ta ƙara second ɗaya rundunar aljani gushshu zata yi sama da su

Ganin iya ta futa yasa itama ta fita a guje har ta buge da garo ɗakin uwani suka shiga suka cure gu ɗaya hakama malam ya zuba ta gumi dan ko shakka babu yasan fatalwar gimbiya ce ta zo musu ba mala'ika ba duk abin da ake yana ji har da hana shi bara

duban mero yayi duk ta fita hayyacin ta sai surutai take allah ya rufawa saminu asiri da yau be ƙwana a idan nan ba

da ya ƙwana da dashi wannan rundunar gushshu zata haɗa domin ai ba zasu bar shi ba saboda kajin mutane da yana sakat a garin nan kullum cikin cin kaji yake suma harya sammu su

*WANNAN KENAN*

"wallahi momcy duk abin da zan ja hankalin sa ina yi amma wallahi a banza anya kuwa yana da lafiya?,

YUSRAH ki nutsu ki gano abin da baya so da wanda yake so shine fa amfanin zaman ki kenan a gidan wallahi na ƙwaɗayin dukiyar gidan alhaji ƙura kin san kaf ƙasar nan ba na biyun su a ƙuɗi da mulki ke ce wacce zata zamo silal dawamar mu a daula kinsan a kullum sai naji ɓakin cikin hajiya turai saboda mahaifin mu ya fi son ta shiyasa har ya bawa bilal auran ta lokacin da na gane haka wallahi har ƙwanciya nayi a asibiti  ƙarshe sai ya haɗani aure da mahaifin ki wanda bashi da wata shahararriyar dukiya  dan haka wallahi ko zan yawo tsirara sai na rusa hajiyan turai akomai

MOMCY yanzu wanne mataki zamu ɗauka naji hajiyan turai tana cewa we waccan shegiyar yarinyar zata dawo gidan nan

ƙwafa tayi tace

"Uhmm zanyi maganin ta  ,

MOMCY ya zanyi ya so ni duk abin da nake kamar baya gani fa

Dariya tayi tace

"YUSRAH  yana kula da komai halin su ɗaya da mahaifinsa zai nuna miki kamar besan komai ba to kisam mummuƙe yake yana lura da komai sannan duk kan wani taƙun kowa yana sa mai ido amma zanje gun bokana Jibi,

"TO bye,

"Bye,

washe gari 🌅

cikin sauri yake komai saboda yau suna da taron jam'iya gashi sauran ƙwana sittin zaɓe wani satin za ai primary election za su yi tsare tsaran abubuwa geznar yasa  blue black tayi mai kyau abinka da farar fata yasa black shoe ga rolex black a hannusa hula ya sa me  tangaran gyara babbar rigar sa yayi ya sai ƙamshi yake zab gawa

ɗauki brief case ya ɗanna remote ya kashe komai na ɓangaran sa cikin nutsuwa yake taka stairs case wayar shi ce tayi ƙara alamun shigowar message be biya ta ƙai ba ya nufi shashin hajiyan turai duk inda yabi sai sojojin nan sun gaishe da shi amsa musu yake cikin sakin fuska

a bakin ƙofar hajiyan turai ya tarar da sam driver sa sam yace

"good morning sir ,

morning sam

ɗur ƙusawa yayi ya amshi brie case ɗin sa

miƙa mai yayi

Cikin hausar sa mara fita yace

"sir ga sabuwar jaridar c.n trues ,

cak ya tsaya be juyo ba yace

innaje office zan duba ta

"sir is very important ,

juyowa yayi ya amsa shafin farko yaga picture ɗin shi anyi rubutu da manyan baƙi

*SHIN KO KUN SAN DALILIN DA YANA ƊAN TAKARAR SHUGABAN ƘASA AZZAM BILAL ƘURA YIN AURE* ✍🏻

*Binta yar jagaliya*

*Oum yasmeen yar mutan yakasai*

Zubawa rubutun ido yayi yawa me shirin gano wani abu wato in kana so ka san asalinka shiga

siyasa rintsai don sa yayi a hankali bakin sa ke furta

*HASBUNALLAHU WANI'IMAL WAKIL*

ba abin da ya ɗaga mai hankali sai we ana zargin sa da yana hurɗa da karuwa shi yasa yaƙi aure ringing ɗin wayar shine ya dawo da shi hayyacin sa da sauri ya ɗauka ganin mahimmancin kira yasa dole ya ɗaga yayi shiru

AZZAM kana dawo wa daga taron jam'iya ka biyo jirgi ka tawo akwai matsala duk da alhmdllh nayi maganin matsalal

to kawe yace mai sukai sallama kai tsaye shiga ciki yayi domin gaishe da hajiya turai sai wanda ya karan ce shi zai gane cewa yana cikin fushi sosai fuskar sa har ja tayi abinka da farin mutum cije leɓansa na ƙasa yayi a rasa da me za ahaɗa shi sai da zina rumtsai ido yayi tambas siyasa mugun wasa ne in baka da juriya ka shigeta sai a haukata ka ba abin da ya tsana ya ƙyamace shi irin zina dai dai ta kansa yayi yayi sallama

cikin fara'a ta am samai yace

"lafiya azzam naga yanayin ka ya sauya wannan fa jaridar da ka duƙunƙune ta me ke faruwa?,

risina wa yayi ya ƙaƙalu murmushin dole  yace

"hajiya bakomai barka da safiya kin tashi lafiya,

ajjiye chokalin hannuta tayi ta dauki tissue ta goge bakin ta ta miƙe cikin nutsuwa take takowa inda yake tace

"Azzam ni na haifeka dan haka kome zakai ka ɓoyemin abin da ke zuciyar ka ni me iya karantar shine ta idonka ko fuskar ka azzam kai ka ɗe muka haifa duk da haka mun baka tarbiya ta gari mun hane ka da yin ƙarya me yasa yanzu xaka fara alhalin fusƙar ka ta nuna ? ,

ƙasa yayi da idanuwan sa jikin sa yayi sanyi ya miƙo mata jaridar amsa tayi ta sami gu ta zauna ga banta ne ya waɗi tayi shiru na wasu sakanni kana tace

"ɗaukaka bata zuwarwa mutum ta cikin sauke dukƙan wata nasara tana zuwa da ƙalubale ba

kowa ne zai yarda da wannan zancan  ƙazafi ne duk wanda yayi maka nasan ubangiji ba zai barsa ba ɗana ƙar ka sa komai a ranka Allah yayi albarka ya dafa maka ,

sosai nasiyar mahaifiyarsa ta shige sa  tambas duk wanda yayi sa'ar uwa ta gari ya dace yace

"hajiya zan tafi taron jam'iya sannan zanje kura baffa na nemana,

okay Allah ya tsare

"ameen yau muzamfar zai dawo na barmai komai na kasuwanci na kafin komai ya dai dai ta,

"To allah ya rufa asiri ya buɗa,

"Ameen ya allah,

miƙewa yayi zai tashi yaji ance

yaya ina ƙwana

be juyoba ciki ciki ya amsa yayi gaba abinsa

haɗiye wani yahu me ɗaci tayi tayi zaman daɓaro a ƙasa kai kace yar borice zuciyar ta tayi wani irin baƙi dan ma Allah ya temake ta hajiya turai ta shiga ɗakin ta sallamar ramlat taji da sauri ta ɗago kai tana jifanta da wata iriyar harara

Mayafi ramlat ta cire tayi ɗamara tace

"wallahi kinsan ni bana ɗauƙar raini ko ? dan wallahi yanzun nan zanyi ƙasa ƙasa da ke banza ƙaruwa ,

cikin zafin nama yusrah ta ɗaga hannu zata mare ta haseena ta tare tace

"ƙarya a kai miki ai yusrah baki ga komai ba sai ance miki yau an daura aure na da yaya azzam
,

Ramlat da zuciyarta ta kawo har huya ta ɗauki takalmin ta ta bugawa haseena abaki tana huci tace

"wallahi kaf cikin ku ni ya azzam ya dace ya aura saboda ni daga dangin ubansa nake kufa yan karan ƙaɗa miya banza ye kawe,

dariya yusrah tayi ta tafa hannaye ta rangaɗa buɗa tace

"anayi muna jin daɗi ku gama haukan ku ni zan aure shi,

sosai bakin haseena ya fashe yana zub da jini dafewa tayi ta zuba uwar ƙara da sauri hajiya turai ta fito tace

"lafiya haseena ramlat yusrah me ya same ki haseena ?"

yusrah tayi carab tace

"faɗa sukai ita da ramlat ta sami gu ta zauna ta kurɓi lemo ta sa earpon a kunnanta tana bin waƙa,

hmmm ni ba zuwanku gidan nan shine matsalata ba aa faɗa kuke ace har yanzu baku girma ba ko wacce a cikin ku da tayi aure da tuni da ƴa'ƴanta wallahi yanzu nan zan ƙira azzam yayi maganin ku nasan beyi nisa ba

Haseena tace

hajiya ɗan allah kiyi haƙuri insha Allah ba zamu ƙara ba

Ramlat kuwa sai hura hanci take domin tare suka tashi da azzam ya bata shekara ukku saboda shi taƙi yin aure yanzu haka tana aiki a asibitin kura ta ɗauki hutu ta tawo nan gu ta samu ta zauna tace

hajiya ki haƙuri insha allah ba zamu ƙara ba yaran nan ne basu da kunya

hajiya turai tace

yusrah ki basu mukullan ɗakuna su zaɓa wannan barin ku gu ɗaya a kwai matsala

wani uban murmushi ta saki me cike da ma'anoni tace

"To hajiya ,

miƙewa tayi ta tashi domin wallahi ba zasu zauna a ɓamgaran nan ba in da ake kai baƙi zata kai su ba har gori sukai mata ba

wannan kenan garin kura

fitowa tayi ta zabga wata uwar hamma ɗakin kahu labahani ta kalla tuni wata dariya ta kubɓuce mata ta dinyi harda ruƙe ciki ganin saminu ya shigo yana waka tayi sauri ta haɗe ranta tace

"ke saminu zo ka siyomin indomi da ƙwai,

washe baki yayi domin yasan in ta aike shi tana yi mai hasafi abin hannunta be rufe mata ido ba yace

"to anty binta gani ,

ɗaki ta shiga ta miƙo mai ATM card ɗinta tace

"kai ma ka siyi ta 500 sauran ka daɗe ,

anty binta bazan  dade ba allah isa kar in sami lahi

Banza tayi mai ta sami gu ta xauna tana yar waka aguje kahu labahani ya fito riƙe da ciki da alama bayi zaishi ga  ɗaga murya tayi tace

"kahu lafiya kake tafiya a ɗur ƙushe?,

wani to tuƙuƙin bakin ciki  ne   ya  zomai  huya  yace

"Binta ƙar de duk abin da akai ki ce baki jiba ?,

Zaro manyan idanuwanta tayi tace

Kahu ban sani ba me akai

banza yayi mata ya shiga ban ɗaki domin gaskiya fatalwar gimbiya su ta raina gashi ta hanashi fita nema  ta tsame yarta a ciki duk ta'asar da binta keyi

ringing ɗin wayarta taji da sauri ta shiga ɗaki ganin sunan alhaji ta saki murmushi domin har ta ganota tana fantamawa da kuɗi hello alhaji

"my beb yau zai zo kura zan toro miki address ɗin sa kije mu gwada sa'ar mu kowa ya dubi halittarki dole ya yaba ,

fari tayi da ƙyawawan idanuwanta tace

"okay toromin amma da sharaɗi inga kuɗina ,

binta shegiyar kaya duk wata hanya da zaki cutu sai kin ƙauce mata

Alhaji kenan ina tare da ku ba dole in koyi fusaha ba ai sai abarni abaya

hakane  my beb yaushe za muyi aurene

"hmmmm alhaji sai na gama cin duniyata da tsinke ,

ni kuma zan baki allurar kidinga tsiƙarar ta

dariya tasa sukai sallama

WANNAN KENAN

shugaban jam'iya yace

mu'azzam zaɓe na ƙaratowa amma banji maganar auran ka ba kasan a tsarin ƙasar nan ba a bawa mara aure  takara mu gashi mun tsayar da kai ƙar ka bamu kunya fa  kowa ya zuba ido yaga yarda zata kaya kuma kasan jam'iyar hamayyah ce ke mulki suna da damar kawar da mu......

*BINTA YAR JAGALIYA*

By

Oum yasmee

Free page ya kusan karewa fa ku hanzarta mallakar naku

Shiru yayi nawasu sakanni yasan gaskiya suka faɗamai amma shi har yanzu be jin zai iya aure domin bega wacce ta kwanta mai a rai ba yace

"Insha Allah zan kawo ƙarshan matsalalnan Allah ya dafa mana,

gabaki ɗayansu suka amsa da amin taro ya watsai fito wa yayi ya sami sam na jiransa ya shiga mota yace me ya kaishi airport domin jirgin 10:45 zai hau gashi goma saura waya ya ɗauka ya kira muzamfar bugu ɗaga ya ɗaga yace

Aslm muzamfar

daga can ɓangaran yace

"wslm gauro ya gari ,

tsadadɗan murmushi shin sa yayi yace

"tsoho ya sanran ka ?,

wallahi azzam shan tablet  ne be ishe ka ba wata ran  zai maka illa nasan ka sani sai ka ƙarar mana da ƙwaiƙwayan mu ko

Lumshe sexy eyes 👀 ɗinsa yayi sai kuma ya fasa ya buɗe yace

A gaskiya muzamfar baka da kunya ya kasuwancin komai na tafiya daidai

"Alhmdllh na rabawa kowa na turo maka da komai ta email sai ka duba ,

Masha allah ina  daughter ta tana lafiya

tana lafiya qalau tace tana so taga ɗan daddy ɗinta

hhhhh ai wannan da ku take ba dani ba  wallahi wayon yarinyar nan yana ban mamaki

wani zancan intayi wallahi cikin mu ƙullewa yake kai ma da tuni kana da yar ka ko ɗanka

"to to sai anjima ai ka haifamin shikkenan ,

be bari yayi magana ba ya kashe wayar ya lumshr idanuwansa ya shiga tunani wanne mataki baffansa ya ɗauka zai kawo ƙarshan matsalalnan ne ko kuwa  me son ɓata mai suna zai ci gaba da ɓata mai suna har suka zo airport be sani ba sai da sam yayi mai magana ajiyar zuciya yasake ya fito ba abin da ya dauko sai brief case ɗin sa kaya ma yana da su a nan ya shiga reception sai nan nan ake dashi masauki ma me kyau a ka bashi kafin jirgin su ya tashi

wannan kenan

"ƙawas ƙwas kina ina ?,

jin muryar rufaida da sauri ta fito daga ɗaki tace

"RUFAIDA sannu da zowa shi go ,

kayan ta ta tattare domin a ƙwai ƙwata a gun tace

wallah ƙawas ni ba zuwa gidan ku ba sai mutum ya ɓaci

wani banzan kallo ta jefe ta da shi tuni ta haɗiye sauran zancan baƙinta

ta sani sarai duk amintar dake tsakanin ta da binta yanzu za aji kan su tace

"Allah ya baki haƙuri ƙawas  ina su kahu naji gidan shiru ko anfita nemane,

kallon ƙofar ɗakin sa tayi tace

"tun safe suna ɗaki har iya me yashin madina ,

haɓa rufaida ta kama tace

"Topa lafiya?,

haɗa rai binta tayi tace

jeki ki tambaye su ta shige ɗakinta

bata da wata da bara ban da ita mata ta  bita domin alƙawari ne ta ɗauƙar wa ƙanta sai ta raba binta da kuɗin nan a komai ta fita ita ta jawota harƙar siyasa amma sun yada ita sun ɗauki binta mutumin da take bala'in so suke ƙwallafa rai a kansa alhaji me tasa yana son binta da aure duk da haryau binta bata san irin alaƙarsu ba  shi da ita

shiga ɗanki tayi ta sami gefen katifar binta ta zauna mayafin da ta ruƙe shi a hannuta ta rataya a huyan ta tace

"ƙawata ashe haka abin alkhairi ya faru ?,

kallon rashin fahimta binta take mata

dafata tayi tace

"zancan yiwa azzam ƙazafi nake nufi,

shiru binta tayi ta saki a jiyar zuciya tace

"rufaida na fasa shigowar ki nake jin wani wa'azi duk da banyi wani karatun addini me zurfi ba nagane ba abu bane me kyau ina tsoran randa ubangiji zai tsayar dani da shi yayi mana hisabi sharrin zina ba ƙaramin sharri bane abin duniya fararrene ƙararre bansan ko ina cikin yin masa sharri in mutu ince da ubangiji me da wanne ido zan kalle shi kina ina shekaran jiya jami'an tsaro har gidan nan suka zo suka tafi dani we yan unguwar nan sun kai musu ƙara zan ɓata yaran su Rufaidah abubuwa summin yawa ga yawan mafarkai marasa daɗi danake,

wani kallo rufaida tayi mata na baki da hankali tace

"BINTU  anya kuwa ba asami wani ko wata sun jefe ki ba domin wallahi wannan maganar da kike kama tayi da wanda aka jefe iya sanina ba ƙyashan ƙwaya anya kuwa  lafiyar ki qalau ƙawata kuɗi fa yanke taƙaicin duniya ,

dan murmushi tayi tace

"Sister wallahi lafiya ta ƙalau kawe yanzu bana son wannan aikin,

Dafa ƙafar ɗarta tayi tace

"Dan girman Allah bintu ki rufa mana asiri ki duba fa ki gani mu muke ci da kanmu sittira gashi kina so ki nemo mahaifin ki in bata wannan hanyar ba ki faɗamin ta ina zamu samu kuɗi har gwarani jikina shine jarina kefa kinƙi sakin jiki ki mori duniyar ki ,

shiru tayi tana auna zancan rufaida tambas ta wannan hanyar ne zata nemo mahaifin ta tunda bata da wani kudi sai wanda yan siyasa in tayi musu posting su bata na kashewa

ganin tayi shiru rufaida tace

"ƙawata tashi muje gidan gwamnati kinsan fa yau muna da taro ko ankusan primary Election ko ?,

ajiyar zuciya ta saki tace

"Eh gobe ne ,

yauwa yar gari tashi yanzu lokacin samun mune yau ba zamu dawo ba sai dare

tashi tayi tace

Bara in shirya gashi wannan yaron be kawo min abin kari ba wallahi tsiyar aiken saminu kenan zani ta dauka ta cire kayan ta

duban ta rufaida tace

"Wallahi bintu da zaki fara harƙar nan zaki sami kuɗi komai naki me kyau ne ,

Wani banzan kallo Binta ta jefe ta dashi tace

"Wallahi wallahi rufaida kika ƙara yimin maganar nan sai nayi maganin ki wato ke kin sulhuntar da naki so kike nima in bayar dashi ba lada sai huya da zunubi ko ,

kwanciya tayi kanta na kallon rufin ƙwano tace

'Allah ya baki haƙuri na dena,

ƙwafa tayi ta fita

Wannan kenan

MU'AZZAM ita siyasa kasuwar buƙata ce  wasu mutanan kana zamane da su bawe dan suna sonka ba a'a sai dan akwai abin da suke nema a gunka lokacin da ya ƙare to zasu gudune su Barka ka kuIa sosai da kowa in AlIah ya baka kujerar nan

sai a lokacin ya iya duban kakan nasa yace

"BAFFA ina tunanin ajiye takarar nan baffa abin har ya kai da yi min ƙazafi lamarin ƙasar nan bashi da lokacin gyaruwa komai an lalata ,

kaf cikin jikoƙina kai na dauko saboda nasan zaka iya zuciyar ka irin tawa ce ko mai nawa naka ne ƙar ka zamo me sarewa kai al'umma ke jira in ka fasa gwiwowin su zasu sare bame iya kuIa da ƙasar su in sukai rashin adalin shugaba wa zai maye gurbin ka sau da yawa muna kuskure amma in muka dawo muna iya gyarawa ina gab da gama binkice akan yarinyar nan

Duban sa yake da manyan idanuwansa yace

"BAFFA wacce yarinya,

Binta yar jagaliya nasa a dinga bibiyar ta ko inta kanta bata sani ba saboda tana da mahimmanci a tafiyar su me tasa dole ta dawo ƙarƙashin iƙon ka bayan mun gama sai mu jefar da ita saboda amfaninta ya ƙare zata iya sawa kujerarka ta waɗi amma in muka ɗauke ta komai yazo ƙarshe bazan yafewa kaina ba inhar ka waɗi saide ban cika me faɗa aji a ƙasar nan ba suwane dadtawan in bamuba su me tasa yarana ne butulcemin sukai

baffa banga amfanin sako mace a cikin siyasar mu ba

tashi yayi ya ɗo gara sandar sa ya fara tafiya yace

zaka iya tafiya ni kaifi ɗaya ne na gama magana duk abin da na ce maka dole kabi bazan taɓa

cutar da kai ba maganar aure kan tana hannu na insha Allah baza kai dana sani da ni ba

yana fadar haka ya shige ciki yabar shi da kallon hanya gun hajiya babba ya shiga domin su gaiyasa sosai tayi murna da ganin jikannata tace

Mijina yau kaine a gari

Zama yayi yace

Hajiyan kura ina huni

"Lafiya qalau ya Maman taka ?"

Tana lafiya tsohuwa

Akwai tsohonwan tuzuru irinka shekaru na ja ba aure anya ba zan zaɓo yarinya in aura maka ba wacce zaka iya haifarta kaga girma ya wadi ko

tanƙwashe kafafunsa yayi yace

"Uhmm kina auramin a ranar zata zama karamar bazzawara ya kikaji wannan zancan,

Muzuba mu gani (next book ɗina )

ba yarda zakai dani wallahi dole ka zauna da ita

Hajiya ina da taro na tafi ki gaida su hajiyan taura

pillow case ta jefu mai tace

Ja'iri anya ba aljana ce ta aure ka ba ana maganar aure sai guduwa

Au tsohuwa baki sani ba ai sunan ta yar mero yafita yana ɗan murmushin

Ya mu'azzam sannu da zuwa

Yauwa jiddah ya Maman taki

Tana lafiya shiga gun hajiya tayi shi kuma ya fita kullum addu'ar ta Allah ya mallaka mata azzam amma ko kallon ta baya yi ......✍🏻

*BINTA YAR JAGALIYA*

By

Oum yasmeen

Ƙarshan free page

Ku hanzarta mallakar ci-gaba.

*BINTA YAR JAGALIYA*

Me suna

*JIFAN GAFIYAR ƁEDU*

(Ba tsuntsu ba farko)

Ku biyoni domin jin harda zata kaya domin kowa yasan

*Ramin kura da wuyar shiga a gayawa kare ya yi hankali*

Ya wasan zai kaya tsakanin mu'azzam da binta yar jagaliya

shirya wa tayi cikin wani lace onion colour an mai ado da flower blue ba wani me tsada bane amma saboda kwalliya ta zauna mata sai ka rantsai me tsada ne anmai dinkin have bubu da strength skirt me tsaka ɗaurinnan tayi ture kaga tsiya ta yafa mayafi a kafada tasa have shoe ta feshe jikinta da turarurruka agogo tasa da sarka tace

"Rufaida taso ba muga ta zama ba ,

tashi tayi ta ɗauki jaƙar ta da wayar ta suka fice tsayawa tayi dai dai ƙofar su iya domin ita wallahi tayi dana sanin abin da tayi musu ta buɗe labule tace

"Uwani kahu saminu zai kawo muku indomie sai kuci yau bani da wani kudi sai wanda zan hau napep ,

idon su a rufe uwani tace

"mun gode binta ,

Kahu kuwa da ƙarfi ya ƙare mai yana jin zancan ci ya taso yace

"Bara in kar ɓo,

karab iya tace

Wallahi labahani kar ka sake ka fita ba fatalwa ta hanaka fita ba kuma in kafi ta balalle mu sami abincin ci ba saboda nasan halinka cinyewa zakai danni yau zan tafi gida

Iya we wacce fatalwa kuke zance

Uhmm yar nan ba za'aji mutuwar sarki a bakina ba

Uwani ce tayi ƙarfin halin kwashe komai ta faɗa mata

Wallahi ku saki idanku ba wata fatalwa

Banza sukai mata dan ba ita za'a yi sama da itaba

Sister kawe ki ƙwace abincin ki tunda sunki yar da kowa yayi harkar gabansa

Kahu labahani yace

"to manna illir khairi irin ku ubangiji ke faɗa shegiya me yawo da fuska yawa ta hoda bahur duk kin kwaye fata jijjiɓar kawe matsamin daga gani ba shakka tauraruwa me wutsiya ganinki ba alkhairi ba hammata duk wari a daure a dinga aski ni wallahi ina tausaya wa masu neman ki yo ubangiji ya kamaki duk warin zina kike,

fuuuuu ta fice yawa kubu buwa dan yasin ta gaji da cin mutuncin da kahun binta yake mata wataran sai ta rama dan tana tsoran binta

Kahu kahu kahu wallahi kaji sau uku nakira Sunan ka kadena ciwa ƙawata munci in kaƙi ba zaka ƙi ganiba su cleaner zan ɗauko maka ku kuma tun kafin in saƙar muku muciji kubuɗe indon ku

ae suna jin haka suka buɗe idon su saidai basu saki jikin suba dan gani suke za ayi sama da su tafiya tayi ganin sun dan warware ta saki ajiyar zuciya ae hakkin sai yayi mata yawa masu majalisar gidan su suna zaune ana zaman banza juyowa tayi zata yiwa rufaida magana taga anliƙa mata poster din azzam cikin bala'i tace

"Wanne dan bura ubanne ya manna min hotan ko dadɗan mutumin nan wallahi yau alo tsiya alo danja ,

ganin ta fara bala'i wani ya taso yace

"Ki haƙuri bara in ɗaye wanine ya manna yau su namatasa zai fito zagaye ,

banza tayi mai ta kama hannun rufaida suka tafi ko da suka je gidan gwamnati a waje suka tsaya suda yan da ba Alhaji ne ya fito yana gyara babbar rigar sa yace

"Yauwa binta ke zaki ja wannan runduna ku watsa taron wannan shegen ƙwaron kai laboss,

Tashi yayi yana lanƙwashe ƙafafuwa yana cije baki yace

"Yess oga gani ,

da ga yau binta ce shugabar ko wanne shege a gidan nan sannan duk wanda a Ka kama karya sake ya ambaci sunana ni zan san yarda na fito da mutum duk da mun hada maki da yan sanda

Angama oga  amma zuciyarsa cike take da haushin binta ko wanne matsayi ta ƙwace musu

Binta ungu ki raba musu ku tafi daga nan inaso yau media ta ɗauka da zancan nan yau kura ba zai bacci ba Insha Allah.

murmushi tayi  tace

"To ,

Mota biyu sukai sosai gari ya cika an kashe tituna domin tarbar sa da yake ya boyar yiyar hanya ya shigo cikin garin har yaje kura ba wanda ya sani
Yana cikin mota yana ɗagowa mutane hannu sosai zuciyarsa take cikin farin ciki ashe ba ƙaramin so suke mai  ba el'bashir ya duba wanda shine mate maƙinsa yace

"Allah ya bani iƙon cikawa al'ummar ƙasar nan burikansu,

Murmushin jindadi yayi yace

"Ameen ya Allah kai me nake gani yan daba suna kaiwa mutanan mu sara,

Cikin sauri ya dubi yan daban tuni mutane suka fara yin ta kansu wasu masu taurin kai na tsayawa cikin sauri ya ɗauki waya domin kiran c.p na yansanda amma har ta katsai be ɗauka ba ƙara ƙira yayi

EL'BASHIR yace

"Bisa duk kan alamu c.p yasan da wannan abun shi yasa yaƙi ɗauka kasan gwamnatin nan bata da imani kafin ya ƙarasa,

ansa madoki an bugemai glass ɗin mota ido biyu sukai da binta wacce taci ɗamara raga raga tayi mai da glass tuni security ɗinsa sukai Kan ta zasu har beta fitowa yayi

Kallonta yayi idanuwanta a tsaye bako tsoron murɗadɗun security ɗin dake kanta sun saita ta da bin diga mace har mace amma ta zubar da kanta shi wallahi rayuwarta tausayi ta bashi tuni yan jaridu suka saita camera Jira ake a ga me zai faru kau da kansa yayi da barin kallon ta yace

"Ku sake ta ƙar ku taɓata ku kununa mata kunsan darajar mace tun da ita bata san ciwon kanta ba kamata yayi ki nutsu ki aure shekarunki ƙanana amma kin biyewa ruɗin duniya ,

yawu ta tofa ya fallatsai mai fuska ta ɗaga murya tace

"Munce bamayi anayi dole ne mazinaci kawe ,

Tuni idanuwansa suka ƙada sukai jaaa yarinya ƙarama ta jefeshi da mugayan kalamai inda yayi

aure da huri da tuni ya haifi kamarta domin bazata huce shekara goma sha takwas ba

handkerchief ya ɗauko ya goge fusƙarsa tuni mutane suka yo kanta ɗaga musu hannu yayi alamun su dagakata matsowa yayi kusa da ita yarda ba wanda zaiji me yace

"Yanzu wasan ya fara ƙarki ga kinyi ban dau ection ba aa ki jira lokacin wasan bazai miki daɗi ba sai na koya miki hankali I well teach youuuuuuuu,

yana kaiwa nan ya shiga mota yace su sake ta jikin ta asanyaye ta koma gidan gwamnati gwamna yace

"Ina tafa miki bisa namijin ƙoƙarin da ke kai zamu baki makafa zuwa gari ya dai dai ta sannan a yanzu zaki ga kuɗin ki zamu baki hannu da hannu saboda gudun matsala ba zamu sa miki ta account ba ,

murmushin jindadi tayi tace

"Nima ina godiya amma kahuna Kar su taɓa shi ,

Alhaji mai tasa yace

"Ƙarki damu ba abinda za su yi mai mu yau kin gama yi mana komai wallahi kin biyamu kina ga har jaridon kasar waje anɗora al'umma ƙasar laimon basa son dan takarar shugaban ƙasa ,

Tuni wani wayo ya zowa rufaida tace

"Saiki bani kuɗin in ajiye miki kafin ki koma normal ko?,

Shiru tayi tace

"Ki saiwa su kahu abinci ki dinga bashi kuɗin cefane ko Allah zai temaka ya bar bara har kaya ki siya musu sannan ki faɗa musu ina lafiya ƙarya damu rabi zan baki sai in ruƙe rabi a hannu na har gida ki siyamini ,

murmushin cimma nasara tayi tace

"Okay ba matsala ,

Sannan dubu ɗari ki ɗauka naki ne

Bayan an sun bawa binta makafa

Wannan kenan

Kahu binta ce ta aiko ni

Kallon hadarin kaji yayi mata yace

Ina jinki bintar da ake cewa an kamata yau ƙwana na ɗaya ina neman ta

kahu binta tana lafiya qalau tace ma in baka dubu hamsin

Keee rufaida bana son hulaƙanci

Wallahi kahu jaka ta buɗe ta ɗauko kudi ta bashi

Buɗa yayi yace

Kuɗin aure ya samu

To ni kahu na tafi

Uhmm ke gaida babarki

Banza tayi mai ta fita domin miliyan ukku binta ta bata tayi take domin har mota ta siya wani gu ta tsaya inda tayi danne danne a waya tace

nazo  ta kashe wayar wani koɗaddan mutumine ya fito yace

Hajjaju iƙon Allah gani an samo gida fa

Glass ta ɗaga tace

"ka samo gidan ?,

washe baki yayi yace

"Na samo amma dubu ɗari biyu,

Yauwa hayar wata zan kama

"Okay ki bada dubu dari kawe ,

Okay muje Ka nunamin

Wanna kenan

Baffa wata alfarma nake son nema

Shiru yayi yace

"Ina jinka Allah isa bata fi ƙarfina ba ,

ƙasa yayi da kansa domin yana ganin Baffa ba lallai ya amince ba da bukatar sa yace

"Bani da wata hanya da zan ƙuntatawa binta sai ta in aure ta in hulaƙanta ta ina ganin zan iya hucewa,

Baffa yace

"Kai ka rasa wazaka aura sai wannan banzar yarinyar zaka jawowa zuri'ar mu abin faɗa mu'azzam sake wata alfarmar ,

Muzamfar yace

"Baffa ka dubu yar da ta kunya tashi a gaban jama'a bashi da hanyar a zai a zabtar da rayuwar ta sai ta wannan ka duba munyi nasara a primary election muna saka ranci tasan sirrin su me tasa sun ɓoye abubuwa da dama ka duba ƙisan mahaifinsa da akai ana zargin suna da sa hannu fa kaga binki can mu zai zamo cikin sauki fa ,

Tambas kunyi tunani me kyau a yau zan yi komai sai kafin nan da ƙwana sittin  mun jefi tsintsu biyu da dutsai daya kaga a idon jama'a ka zama mai aure sai dai mu muka san manufar yinsa

Wannan kenan

Murna take tunda komai ya lafa yau zata kwana a gidan ta kwashe komai nata tayi ta fito ita da rufaida shiga motar ta tayi ta fara tuƙi tace

Wallahi rufaida yau jina nake wani sa kayau nasan de yanzu ya haƙura ya zubar da makamansa

Uhmm Allah yasa

Ameen kin mai da su kahu

"Eh jiya suka koma ,

Gaban makeƙen gidan suka tsaya sosai binta tayi mamakin arahar gidan tayi farinciki sosai sai ma da ta shiga taga an zuba komai yanzu jibi zata fara binkican mahaifinta kahu yayi murna da ganinta sai nan nan suke da ita shi da uwani zama tayi tana ƙarƙada ƙafa tace

"To yanzu kahu komai ya sauya Banda fita bara ,

toto nadena binta

Uwani

gyara zanin ta tayi tace

"Na'am binta,

Banda sana'a ina da kuɗin ciyar da ku

to bazan sake ba

kawata ni zan tafi

Okay muje in raka ki ko

Tashi tayi su ka fita

Tashi yayi shima ya dubi uwani yace

Ni zan fita in zaga gun yan uwa daula ta samu

To me gida sai kadawo

Dariya yayi yace

Rabon kiyimin wannan tarbar tun muna cin amarci

Ae yanzu komai ya huce

Babbar riga ya gyara ya fita tafiya ya fara wata ƙatuwar jeep ce ta tsaya baƙa wasu burɗadɗun mutane ne suka fito suka ce

Tsoho shiga

Ja da baya ya fara ji yayi ya jingina da wani garo juyowa yayi ashe mutum ne yace

"Lafiya ,

Ka yiwa kanka arziki ka shiga tambaya zaka amsa mana

Ba yarda ya iya yace

"To ba yarda ya iya ya bisu tafiya sukai mene sa tu kunna su ka je gidan gona duk bishiyo fitowa sukai suka tisa ƙeyarsa har wani har wani hadaddan floor  wanda shi ake kira da aljannar duniya zama yayi a ƙasa suka fita suka jawo ƙofa

Hawaye ne ya fara zubomai ya gashi a fadar aljanu shi daman ya san ba zasu barshi ba tafiya yaji

Zabura yayi ganin mutumin da yake gani a poster

Murmushi ya sakar mai ya zauna yace

Bisimillah zauna cikin aminci

Murza idonsa yayi yace

Nan ma ya isa

Okay wata alfarma nake nema

Anya kuwa ni Iabahani ba mafarkin da nasa ba naka ba

Ido biyu kake zauna dan Allah

"To to zama yayi ,

Kai haƙuri na sa an dauko ka

Bakomai ka isane

Yauwa Nagode ina nemawa jikana auran yar wajanka ina fatan ba ai mata miji ba

Washe baki yayi me ragaje tayi goshi yace

"A'a ban mata ba Maryam a kwai ƙirkir wallahi tafi Binta komai,

ganin be gane wacce yake nufi ba ya danna wani majigi nan hotan Binta ya bayyana yace

"Wannan nake nufi,

Zaro ido yayi yace

"Binta tafi ƙarfina wallahi ga Maryam nan na baku ita nake da iko a kanta,

Kar ka damu aikai wakilinta ne zamu san yarda za a Kaita gidan a ɓoye sai dai ta farka ta ganta a gidan su  zan kai ka Makka sannan zan baka ƙaton gida kai  shiru da bakin ka

Zama ya gyara yace

"To to Ni wallahi yanzu a shirye nake na baku ita yanzu muje masallaci a daura,

Murmushi yayi yace

Angon baya ƙasar nan amma nine wakilinsa ga abokin sa zai zo a yau zan baka komai da nayi maka alƙawari za a dauki komai a nuna mata dan ya zama sheda.......✍🏻